# Aƙidar

# 'Yan Shi'a

# dangane da

# Sahabbai

Umar Labɗo

# بسم الله الرحمن الرحيم

'Yan Shi'a suna ƙudure gaba da ƙiyayya mai tsanani da jafa'i da nunƙufurci da mugun alkaba'i ga Sahabban Annabi (SAW), Allah ya yarda da su baki ɗaya. Littafansu na da, da na yanzu, suna cike da mummunan suka da zagi da cin zarafi da shiga irili ga waɗannan zaɓaɓɓun bayin Allah waɗanda Allah ya zaɓe su a matsayin waziran Manzonsa don su taimaka masa iyar da aikensa.

## *Sahabbai Sun Yi Ridda!!*

'Yan Shi'a suna ƙudure cewa Sahabbai baki ɗayansu sun yi ridda kuma sun kafirta sai kaɗan daga cikinsu. Babban malaminsu a fannin ruwaya, wanda suke ɗaukar sa kamar yadda muka ɗauki Bukhari a fannin Hadisi, watau Muhammad binu Ya'aƙub Alkulaini, ya karɓo ruwaya daga Abu Ja'afar (Imamin Shi'a na biyar) wai ya ce, "Mutane baki ɗaya sun yi ridda bayan Annabi (SAW) sai mutum uku kawai. (Mai ruwaya ya ce) sai na ce: Su waye mutum ukun? Ya ce: Miƙdad binul Aswad da Abu Zarrin Algifari da Salman Alfarisi."[1]

Amma mene ne dalilin wannan tsatssauran hukunci a kan zaɓaɓɓun halitta bayan Annabawa da Manzanni? Mene ne dalilin da ya sa 'yan Shi'a suke kafirta Sahabbai? Dalilan guda biyu ne rak, ba daɗi ba ragi. Na ɗaya shi ne faɗinsu cewa wai Manzon Allah (SAW) ya yi wasiya cewa Ali binu Abi Ɗalib(RA) ne zai zama khalifa a bayansa amma sai Sahabbai suka ƙi ƙemadagas su zartar da wannan wasiya. Maimakon haka sai suka naɗa

[1] A duba **Alraudatu minal Kafi** na Kulaini, Darul Kutubil Islamiyya, Tehran-Iran, ba tarihi, mujalladi na 8, shafi na 245-246.

Abubakar ya zama khalifa kuma daga bayansa suka naɗa Umar da Usman. Sai a karo na huɗu ne aka baiwa Ali(RA) wannan matsayi.

Dalili na biyu, a lokacin da fitina ta taso a tsakanin al'umma sakamakon kisan gila da aka yi wa Sarkin Musulmi Usman(RA), yaƙi ya auku a tsakanin Sarkin Musulmi Ali(RA) da jama'arsa a hannu guda da kuma Ɗalha da Zubair da Aisha, Allah ya yarda da su, tare da magoya bayansu a ɗaya hannun. 'Yan Shi'a suna ganin waɗan nan Sahabbai sun yaƙi Ali(RA) a bisa zalunci. To da waɗannan dalilai biyu ne 'yan Shi'a suke kafirta Sahabbai: hana Ali(RA) khilafa a farkon rasuwar Annabi (SAW) da kuma yaƙi da shi a zamanin khalifancinsa.[1]

## *Sahabbai Ne Mafi Sharrin Mutane!!*

Aƙidar 'yan Shi'a dangane da Sahabbai ba ta tsaya a kan kafirta su ba kawai, amma suna ganin cewa su Sahabbai su ne mafiya sharrin halittar Allah, wall iyazu billah!! Kuma suna ƙudure cewa imani da Allah da Manzonsa ba ya tabbata sai an barranta daga gare su, musamman dai manya-manya daga cikinsu kamar Abubakar da Umar da Usman da Aisha da Hafsa da sauran ire-irensu. Muhammad Baƙir Almajlisi, ɗaya daga cikin manyan malaman Shi'a, yana cewa: "Aƙidarmu ta barranta ita ce cewa mu muna barranta daga gumaka huɗu: Abubakar da Umar da Usman da Mu'awiya; da kuma mataye huɗu: Aisha da Hafsa da Hindu da Ummul Hakam. Kuma muna barranta daga dukkan mabiyansu da magoya bayansu; kuma muna ƙudure cewa su ne mafiya sharrin halittar Allah a bayan ƙasa; kuma cewa

[1] Duba **Awa'ilul Maqalat** na Muhammad binu Muhammad binu Nu'uman Almufid, bugun darul Kitabil Islami, Bairut, 1403/1983, shafi na 45; da **Al'anwarun Nu'umaniyya** na Ni'imatullahi Aljaza'iri, bugun Madba'atu Bab, Tibriz-Iran, ba tarihi, mujalladi na 2, shafi na 244.

imani da Allah da Manzonsa da Imamai ba ya tabbata sai bayan an barranta daga maƙiyansu (yana nufin Sahabbai)."[1]

'Yan Shi'a suna nuna ƙiyayya ta musamman ga Sarkin Musulmi Umar binul Khaɗɗabi(RA). Daga cikin irin ruwayoyin da suka keɓe masa shi kaɗai akwai abinda wani malaminsu mai suna Ni'imatullahi Aljaza'iri ya ruwaito. Ya ce, "Abinda yake ɗaure kai shi ne, yaya Ali (A.S) ya aurawa Umar binul Khaɗɗabi (diyarsa) Ummu Kulthum, alhali kuwa miyagun ayyuka sun bayyana daga gare shi kuma ya yi ridda ga barin addini sama da riddar duk wani mai ridda. Har ma ruwayoyi sun taho da cewa (ranar Alƙiyama) za'a yiwa Shaiɗan ƙuƙumi da sasari saba'in na baƙin ƙarfen Jahannama sa'an nan a ja shi zuwa ga taron hisabi. Sai ya duba gabansa, sai ya ga wani mutum mala'ikun azaba suna kora shi, an ƙuƙumce shi da sasari ɗari da ishirin na Jahannama. Sai Shaiɗan ya kusanto shi ya ce: Me mara rabo ya yi har ya fi ni azaba, alhali ni na ɓatar da halitta baki ɗaya, na kai su ga halaka? Sai Umar ya ce da Shaiɗan: Ba abinda na yi sai dai na ƙwace wa Ali binu Abi Ɗalib khilafa. Ga alama yana ganin ƙanƙantar abinda ya aikata; bai sani ba cewa duk abinda ya faru a duniya na kafirci da zalunci, ya auku ne a dalilin wannan aika-aika tasa."[2]

Duba ka gani, ɗan uwa mai karatu, yadda 'yan Shi'a suke ɗaukar cewa wai Umar(RA) ya fi Shaiɗan tsananin azaba a Lahira, kuma duk abinda ya faru a duniya na kafirci da zalunci a dalilinsa ne!!

---

[1] A duba **Haqqul Yaqin** na Muhammad Baqir Majalisi, bugun Muassasatul Wafa, Bairut, ba tarihi, shafi na 519.

[2] Duba **Al'anwarun Nu'umaniyya,** mujalladi na 1, shafi na 81-82.

## *Kazafin 'Yan Shi'a ga Sahabbai*

'Yan Shi'a suna yin ƙazafi ga manyan Sahabbai da matan Manzon Allah(SAW) Uwayen Muminai, Allah ya ƙara yarda a gare su baki ɗaya. Kuma wannan yana cikin littafan manyan malamansu waɗanda suke izna da su. Ga ɗan misali:

1. Kazafinsu ga Umar binul Khaɗɗabi(RA). Wannan babban Sahabi na Annabi(SAW) yana cikin mutanen da Rafilawa suka fi ƙi, saboda haka sun yi masa ƙazafi mai yawa. Wanda ya fi shahara daga cikin ƙazafinsu gare shi, shi ne abinda malaminsu ɗan hayaƙi, Ni'imatullahi Aljaza'iri, ya ruwaito, ya ce, "Umar binul Khaɗɗabi ya kasance yana da wani ciwo a duburarsa (idan ya motsa) babu abinda yake sanyaya shi sai ruwan maza."[1] Inna lillahi wa inna ilaihi raji'un! Sai mai karatu ya gafarce mu saboda naƙalto wannan ɗanyar magana wacce da a ce an dangana ta ga kafiri ne da bai kamata a faɗe ta ba haka gatse-gatse. To sai dai malaman Rafilawa, waɗanda a haƙiƙa su Majusawa ne, zancen batsa ba wani abu ba ne a wajen su. A taƙaice dai, mai karatu ya ga yadda 'yan Shi'a suke jifan Sayyidina Umar(RA) da liwaɗi a fili, ƙarara, tare da amfani da ƙazaman kalmomi da miyagun lafuzza irin waɗanda ba mai iya amfani da su sai su.

2. Kazafinsu ga Usman binu Affan(RA). Ni'imatullahi Aljaza'iri, har yau, ya ruwaito, ya ce, "Usman ya kasance yana daudu, kuma ya zama ana wasa da shi."[2] Wannan shi ma jifa ne da liwaɗi ga wannan babban bawan Allah, tsarkakakke, mai kunya da kamun kai, surukin Annabi, wanda Manzo(SAW) yake jin kunyar sa, kuma mala'iku ma suke jin kunyar sa.

3. Kazafinsu ga Innar Muminai A'isha(RA). Ummul Muminina, wacce malamin Shi'a, Ali Al'amili Albayali, yake kiran ta **ummul shururi**[3] (uwar sharrurruka!) ba ta tsira ba daga ƙagen Rafilawa da ƙazafinsu. Har yau har gobe suna gaskata ƙazafin da munafikai suka yi mata a zamanin Annabi(SAW), inda suka jefe ta da alfasha, wanda kuma Allah Maɗaukaki ya barrantar da ita, ya kuɓutar da ita daga wannan zargi. Amma 'yan Shi'a

---

[1] **Al'anwarun Nu'umaniyya** na Ni'imatullahi Aljaza'iri, mujalladi na 1, shafi n 63.

[2] **Al'anwarun Nu'umaniyya,** mujalladi na 1, shafi na 65.

[3] A cikin littafinsa, **Assirudul Mustaqim ila Mustahiqqi Attaqdim,** bugun Madba'atul Haidari, Bairut, ba tarihi, mujalladi na 3, shafi na 161.

ba su gamsu ba; ba su yarda da ayoyi goma sha takwas da Allah ya saukar a cikin Suratun Nuri ba domin barrantar da ita. Suna ganin waɗannan ayoyi mahaifinta Abubakar ne ya soka su cikin Alƙur'ani don ya wanke sunan ɗiyarsa, amma ba Allah ya saukar da su ba. Don haka suke ci gaba da laƙa mata wannan zargi. Har ma suna faɗin, idan Mahadinsu ya bayyana a ƙarshen zamani zai fito da ita daga kabarinta ya tsayar mata da haddi.[1]

Kafircin da yake cikin wannan magana ba'a ɓoye yake ba. Domin kuwa, bayan ƙaryata Alƙur'ani ƙarara, da ƙazafi ga wannan babbar baiwar Allah, matar Annabi a duniya kuma matarsa a aljanna, maganar har yau tana nuna suka da zargi ga Annabi(SAW) cewa shi bai tsayar mata da haddi ba. Allah ya kiyashe mu taɓewa!

4. Kazafinsu ga Muhammad binu Ali binu Abi Ɗalib. Kazafin 'yan Shi'a har da jinin Ali(RA) bai bari ba domin sun jefi wannan ɗa nasa, watau Muhammad binul Hanafiyya, da zina.[2]

Kiyayyar 'yan Shi'a ga Sahabban Annabi ta kai matuƙa har suka halasta la'antar su. Sun ma ɗauki la'antar Sahabbai a matsayin ibada wacce suke neman kusanci ga Allah da ita!! Kuma ko a cikin Sahabban ma, ƙiyayyarsu ta fi tsanani ga shugabanninsu mafifita: Abubakar da Umar. Duba wannan ruwaya, wacce wani malaminsu mai suna Mulla Kazim ya naƙalto, yana dangana ta BISA KARYA ga Ali Zainul Abidin binu Hussain binu Ali binu Abi Ɗalib, Allah ya ƙara musu yarda. Ya ce: Abu Hamza Althumali ya karɓo daga Ali Zainul Abidin cewa ya ce, "Wanda ya la'anci Jibtu da Ɗagutu (yana nufin Abubakar da Umar) la'ana guda, Allah zai rubuta masa lada dubu sau dubu, ya kankare masa zunubi dubu sau dubu kuma ya ɗaukaka masa daraja dubu sau dubu saba'in. Kuma wanda ya la'ance su da yammaci la'ana guda, za'a rubuta masa kamar haka. (Mai

[1] A duba **Tafsirul Qummi** na Ali binu Ibrahim Alqummi, bugun Darul Kitab, Kum-Iran, 1387 B.H. mujalladi na 2, shafi na 377.

[2] Duba labarin a cikin **Furu'ul Kafi** na Kulaini, *Kitabul Hudud,* bugun Darul Kutubil Islamiyya, Bairut, 1375 B.H., mujalladi na 7, shafi na 187.

ruwaya) ya ce: Sai shugabanmu Ali binu Hussaini ya wuce (bayan ya faɗi wannan magana, ni kuma) sai na shiga wurin shugabanmu Abu Ja'afar Muhammad Albaƙir na ce masa: Ya shugabana, wata magana ce na ji daga mahaifinka. Sai ya ce: Faɗe ta mu ji, ya Thumali. Sai na maimaita masa maganar. Sai ya ce: Haka take, Thumali! Ko kana so in yi maka ƙari? Sai na ce: E, ya shugabana. Sai ya ce: Wanda ya la'ance su la'ana guda a ko wace safiya ba za'a rubuta masa zunubi ba a wannan wunin har zuwa yammaci, kuma wanda ya la'ance su la'ana guda da yammaci ba za'a rubuta masa zunubi ba har ya wayi gari."[1]

Banda wannan ma, akwai addu'o'i na musamman waɗanda aka wallafa su, aka tsara su, waɗanda kuma suka ƙunshi la'ana da tsinuwa da miyagun lafuzza ga waɗan nan manyan Sahabbai: Abubakar da Umar, Allah ya ƙara musu yarda, waɗanda yan Shi'a suke yin wurdi da su, suna maimaita su safe da yammaci kamar yadda Musulmi yake maimaita ***Ayatal Kursiyu*** da ***Amanar Rasulu*** da ***Laƙada Ja'akum!!***

Daga cikin addu'o'in akwai wata da suke kira Du'a'u Sanamai Kuraishin, watau Addu'ar Gumakan Kuraishawa Biyu, suna nufin Abubakar da Umar, Allah ya ƙara musu yarda. Ga yadda addu'ar take a Larabci, kafin daga baya mu kawo fassararta:

***"Allahumma Salli ala Muhammadin wa Ali Muhammadin, wal'an Sanamai Kuraishin wa Jibtaihima wa Ɗagutaihima wa ifkaihima wa ibnataihima allazaini khalafa amraka, wa ankara wahyaka, wa jahada in'amaka, wa asaya Rasulaka, wa ƙallaba dinaka, wa harrafa kitabaka….. Allahumma il'anhuma fi maknunis sirri, wa zahiril alaniya, la'anan kathiran abadan, da'i'man sarmadan, la inƙiɗa'a li amadihi, wa la nafaza li adadihi, la'anan ya'udu awwaluhu wa la yaruhu akhiruhu, lahum wa li a'awani him,***

[1] Duba **Ajma'ul Fada'ihi** na Mullah Kazim, shafi na 513.

***wa ansari him, wa muhibbi him, wal muƙtadina bi ƙalami him, wal musaddiƙina bi ahkami him…. Allahumma azzib hum azaban yastagithu minhu ahlun nari, amin ya Rabbal Alamin.”***

Ma’anar addu’ar: “Ya Allah ka yi daɗin tsira ga Muhammad da alayen Muhammad. Kuma ka la’anci gumakan Kuraishawa biyu, da jibtinsu da ɗagutunsu, da ƙarerayinsu da ɗiyansu mata biyu. Waɗanda suka saɓa umarninka, suka yi musun wahayinka, suka butulce ma ni’imarka, suka juya addininka, suka sauya littafinka…. Ya Allah ka la’ance su a cikin ɓoyayyen sirri da zahirin dake sarari, la’ana mai yawa ta har abada, madauwamiya ta dun-dun-dun, wacce babu yankewa ga nisanta kuma babu ƙarewa ga adadinta, la’ana wacce farkonta zai riƙa komowa kuma ƙarshenta bai tafiya, gare su da masu mara musu da mataimakansu da masu ƙaunarsu da masu koyi da maganarsu da masu gaskatawa da hukunce – hukuncensu….. Ya Allah ka yi musu azaba, azabar da ‘yan wuta za su riƙa neman tsari da ita, amin ya Ubangijin Talikai.”[1]

Har yau, akwai wata addu’ar la’ana mai lugude, wacce ta ƙunshi la’antar magabata guda tara, waɗanda suka haɗa da Sahabbai da Tabi’ai, tare da maimaita la’ana ga Umar binul Khaɗɗabi(RA) sau tara. Ga yadda lafazin addu’ar yake:

***Allahumma il’an Umara, thumma Ababakarin wa Umara, thumma Usmana wa Umara, thumma Mu’awiyya wa Umara, thumma Yazid wa Umara, thumma Ibna Ziyadin wa Umara, thumma Ibna Sa’adin wa Umara, thumma Shamran wa Umara, thumma Askara hum wa Umara. Allahumma***

[1] Domin ganin wannan mugunyar addu’a, sai a duba **Miftahul Jinan fil Ad’iyati waz Ziyarati wal Azkar**, ba’a san marubucinsa ba, bugun Maktabatul Mahuri, Bahrain, ba tarihi, shafi na 113-114.

***il'an A'ishata wa Hafsata wa Hindan wa Ummal Hakam. Wal'an man radiya bi af'ali him ila yaumil ƙiyamah.***[1]

Ga ma'anar addu'ar: Ya Allah ka la'anci Umar, sa'an nan Abubakar da Umar, sa'an nan Usmanu da Umar, sa'an nan Mu'awiyya da Umar, sa'an nan Yazidu da Umar, sa'an nan Ibnu Ziyad da Umar, sa'an nan Ibnu Sa'ad da Umar, sa'an nan Shamru da Umar, sa'an nan Askar nasu da Umar. Ya Allah ka la'anci A'isha da Hafsa da Hindu da Ummul Hakam, kuma ka la'anci (duk) wanda ya yarda da ayyukansu har ya zuwa ranar Alƙiyama.

Wannan babbar addu'a, kuma mugunya, ta 'yan Shi'a tana bukatar darasu. Da farko dai bari mu bi sunayen da suka zo a cikinta domin mu san su waye. Abubakar da Umar da Usmanu da Mu'awiyya, Allah ya ƙara musu yarda, ba sa bukatar bayani; kowa ya san su. Haka nan A'isha da Hafsa. Yazidu kuwa shi ne ɗan Mu'awiyya wanda ya gaje shi a mulkin daular Musulunci, kuma wanda a zamaninsa ne aka kashe Hussaini(RA). Ibnu Ziyad shi ne gwamnan Kufa a zamanin mulkin Yazidu, kuma rundunarsa ce ta kashe Hussaini(RA). Shi kuwa Ibnu Sa'ad (sunansa Umar binu Sa'ad binu Abi Waƙƙas) shi ne kwamandan rundunar da ta kashe Hussaini(RA).[2] Shamru ban san shi ba; ban gane wanda suke nufi da shi ba. Ga al'adar Rafilawa idan suka yi amfani da kalmar Askar to A'isha suke nufi da ita, saboda raƙumin da ta hau a yaƙin Jamal sunansa Askar. Kuma da yake an ambace ta da suna a cikin addu'ar, muna iya ɗauka cewa ita ma an ninka mata la'ana ne saboda tsananin ƙiyayya, kamar yadda aka ninninka wa Umar(RA). Hindu kuwa ita ce mahaifiyar Mu'awiyya(RA) kuma Ummul Hakam ita ce kakar Marwan binul Hakam, uban yawancin khalifofin Banu Umayya, ciki har da Umar binu Abdil'aziz khalifa mai adalci, Allah ya yi masa rahama.

Dalilin la'antar waɗannan manyan bayin Allah a wajen 'yan Shi'a abu ne mai sauƙi. Su dai Abubakar da Umar da Usmanu, Allah ya ƙara musu yarda, laifinsu a wajen Rafilawa shi ne wai sun hana Ali binu Abi Ɗalib khilafa, kuma sun hana ma Faɗima(RA) gado na gonar da mahaifinta

---

[1] A duba **La'ali'ul Akhbari** na malaminsu Muhammad Attursirkani, bugun Qum-Iran, ba tarihi, mujalladi na 4, shafi na 92.

[2] Domin bayanin hakikanin rawar da Yazidu da Ibnu Ziyad da Ibnu Sa'ad suka taka wajen shahadar Hussaini(RA) a Karbala, sai a nemi littafinmu **Wa Ya Kashe Hussaini?** bugun Zomo Press, Kaduna, 2010.

Annabi(SAW) ya bari. Ita kuma A’isha(RA) ta yi faɗa da Ali a Yaƙin Jamal. Hafsa(RA) ba ta yaƙi Ali ba, kuma ba ta yi ma Faɗima kome ba. Don haka muna iya ɗauka cewa wata ƙila ƙiyayyar ubanta, Umar binul Khaɗɗabi, ce ta nashe ta, ta ja mata wannan la’ana. Mu’awiyya kuwa, Allah ya ƙara masa yarda, shi ne uban masu laifi, a ganin Rafilawa, domin shi ya yaƙi Ali kuma ya tankwaɓe masa khilafa a bayan da ya same ta. Kuma wannan babban laifi nasa shi ya shafi mahaifiyarsa, Hindu. Ummul Hakam, kakar Marwan binul Hakam, ‘yan Shi’a suna ɗauka cewa wai jikanta, Marwan, shi ne ya zuga Usmanu ya yi gaba da Ali. Kuma ga shi jikokinsa sun yi ta more mulki, suka hana jikokin Ali ɗanawa. Su kuwa Yazid da Ibnu Ziyad da Ibnu Sa’ad su suka kashe Hussaini(RA). Wannan ita ce aƙidar Rafilawa da fahimtarsu, kuma ita ta sa suke la’antar waɗannan manyan bayin Allah ba dare ba rana.[1]

Abinda ya gabata a nan ɗan misali ne kawai na gabar ‘yan Shi’a da ƙiyayyarsu ga zaɓaɓɓun wannan al’umma, watau Sahabban Annabi (SAW), Allah ya ƙara musu yarda baki ɗaya. Kuma wannan gaba haka take tun ran da maƙiyin Allah, Abdullahi binu Saba’i Bayahude, ya kafa wannan ƙungiya ta Shi’a har zuwa yau. Haka nan, a kan wannan aƙida ne su ma ‘yan Shi’a na wannan zamani suke. Bari ka ji abinda shugabansu kuma babban malaminsu na wannan zamani, watau Ayatullahi Khumaini, yake faɗi. Ya zo a cikin littafinsa ***Kashful Asrar*** kamar haka: “Mu a nan babu ruwanmu da tsofaffi biyu (yana nufin Abubakar da Umar) da abinda suka aikata na saɓawa Alƙur’ani, da wasa da suka yi da hukunce-hukuncen Allah, da abinda suka halasta ko suka haramta daga ƙashin kansu, da abinda suka aikata na zalunci a kan Faɗima ɗiyar Annabi (SAW), da kuma sauran ‘ya’yansa. Sai dai mu a nan, muna nuni ne zuwa ga jahilcinsu da hukunce-hukuncen Allah da addini.”[2]

[1] Domin darasun ra’ayin Ahalus Sunna dangane da wannan aqida da fahimta ta ‘yan Shi’a, sai mai karatu ya nemi littafinmu, **Wa Ya Kashe Hussaini?**

[2] **Kashful Asrar** na Ayatullahi Khumaini, bugun Daru Amar, Omman-Urdun, 1408/1987, shafi na 126.

Duba ka gani, ɗan uwa mai karatu, wai Khumaini ne yake dangana jahilci da zalunci ga Sahabban Annabi(SAW): Abubakar da Umar, Allah ya ƙara musu yarda!!

Kuma har yau, Khumaini ya zargi Sayyidina Abubakar da Sayyidina Umar, Allah ya ƙara musu yarda, da cewa wai sun sauya Alƙur'ani!! Ya ce, "Lallai Allah ya ambaci nau'in mutane takwas waɗanda suka cancanci rabo a cikin zakka, amma sai Abubakar ya jefar da nau'i guda daga cikin waɗannan nau'o'in mutane bayan da Umar ya zuga shi ya yi haka."[1]

Sa'an nan daga bisani, ya jefa wa Sahabbai baki ɗayansu kalmar kafirci. Wal iyazu billah!! Ya ce, "Babu shakka su (Sahabbai) sun baiwa Annabi haƙƙinsa yadda ya kamata!! (yana yi musu ba'a ne). Annabi wanda ya wahala, ya sha fama, kuma ya jure dukkan musifu domin shiryar da su, sa'an nan ya cika (a lokacin rasuwarsa) alhali yana jin kalmomin Ɗan Khaɗɗabi waɗanda aka gina a kan kafirci da zindiƙanci."[2]

Wannan mugunyar aƙida a kan ta ne 'yan Shi'ar Nijeriya suke, kamar yadda muka sha ji da kunnuwanmu, kuma muka sha gani da idanunmu. Sai dai sau da yawa su kan ɓoye ta ga mutane saboda Taƙiyya, watau munafurci da yaudara!! Muna roƙon Allah Maɗaukaki ya shirye su, ya arzuta su da kyakkyawar tuba kafin zuwan ajalinsu. Mu kuma, Allah ya shiga tsakanin mu da su, ya tsare mu daga ƙudure aƙidarsu.

## Falalar Sahabban Annabi(SAW)

Sahabban Annabi (SAW), Allah ya ƙara yarda a gare su, ba sa buƙatar mu yi wani bayani domin kuɓutar da su da barrantar da su daga abin da 'yan Shi'a suka dangana musu na kafirci da ridda da zalunci; saboda babu wani

[1] **Kashful Asrar** na Khumaini, shafi na 131.
[2] Duba **Kashful Asrar** na Khumaini, shafi na 137.

mai da'awar Musulunci da yake shakkar imaninsu, da ɗaukaka, da falalarsu, sai fa wanda Allah ya makantar da basirarsa, ya ɓatar da shi.

Amma za mu kawo wasu ayoyi na Alƙur'ani waɗanda suke nuna falalar Sahabbai kuma suna tabbatar da cewa ƙudure aƙidar 'yan Shi'a dangane da waɗan nan manyan bayin Allah ƙaryatawa ne ga Alƙur'ani, kuma ƙaryata Alƙur'ani, kamar yadda kowa ya sani, kafirci ne.

**Allah ya tabbatar da imanin Sahabbai:** Ya ce, "Kuma waɗanda suka yi imani kuma suka yi hijira, kuma suka yi jihadi a cikin hanyar Allah, kuma da waɗanda suka bayar da masauki kuma suka yi taimako, waɗannan su ne muminai da gaskiya, suna da gafara da wani abinci na karimci. Kuma waɗanda suka yi imani daga baya, kuma suka yi hijira kuma suka yi jihadi tare da ku, to, waɗannan daga gare ku suke." (Suratul Anfal: 74-75).

A cikin aya ta farko, Ubangiji ya yi bayanin waɗanda suka yi imani kuma suka yi hijira (waɗannan su ne Muhajiruna), da kuma waɗanda suka bayar da masauki ga masu hijirar (su ne Ansar), ya tabbatar da cewa su ne muminai na gaskiya. Waɗannan kungiyar mutane biyu, Muhajiruna da Ansar, su ne Assabiƙunal Auwaluna: Sahabbai waɗanda suka yi rigaye wajen shiga Musulunci, imaninsu da rigayensu sun tabbata, kuma wanda duk ya shiga Musulunci daga bayansu yana biye da su ne.

**Allah ya tabbatar da tsarkin zukatan Sahabbai da ihlasinsu:** Ya ce, "Muhammadu Manzon Allah ne. Kuma waɗannan dake tare da shi masu tsanani ne a kan kafirai, masu rahama ne a tsakaninsu, kana ganin su suna masu ruku'i masu sujada, suna neman falala daga Ubangijinsu da yardarsa." (**Suratul Fathi**: 29). Kuma ya ce, "(Ku yi mamaki) ga matalauta masu hijira waɗanda aka fitar daga gidajensu da dukiyoyinsu, suna neman falala daga

Allah da kuma yarda, kuma suna taimakon Allah da Manzonsa. Waɗannan su ne masu gaskiya." (**Suratul Hashri**: 8).

**Allah ya tabbatar da fifikonsu:** Bayan Ubangiji ya tabbatar da imanin Sahabbai da tsarkin niyyarsu, kuma ya tabbatar da fifikonsu ba kawai a kan wannan al'umma ba, a'a har ma da sauran al'ummai. Ya ce, "Kun kasance mafi alherin al'umma wadda aka fitar ga mutane, kuna umarni da alheri kuma kuna hani daga abinda ake ƙi, kuma kuna imani da Allah" (**Suratu Ali Imrana**: 110). Imam Ibnu Kathir ya ce, "Wannan aya tana nufin dukkan al'umma, amma kuma mafifita a cikin wannan al'umma su ne na farkonta."[1] Har yau, Allah Mɗaukaki yana cewa, "Kuma kamar wannan, muka sanya ku al'umma matsakaiciya (mafificiya, adala) domin ku kasance masu bayar da shaida a kan mutane." (**Suratul Baƙara**: 143). Wannan aya ita ma ma'anarta kamar ta farko ce.

**Allah ya yi gafara ga Sahabbai tare da Annabi:** Ubanjigi Maɗaukaki ya ce, "Lallai ne, haƙiƙa, Allah ya karɓi tubar Annabi da Muhajirina da Ansar waɗanda suka bi shi, a cikin sa'ar tsanani, daga bayan zukatan wani ɓangare daga garesu sun yi kusa su karkata, sa'an nan (Allah) ya karɓi tubarsu. Lalle shi ne mai tausayi, mai jin ƙai gare su." (**Suratut Tauba**: 117). Ma'anar ya karɓi tubarsu shi ne ya yi musu gafara. To idan Allah ya yi musu gafara, ya wani zai ce sun kafirta, ko sun yi ridda, ko sun yi zulunci?!!

**Allah ya yarda da Sahabbai:** Ubangiji Maɗaukaki ya ce, "Kuma magabata na farko daga Muhajirina da Ansar da waɗanda suka bi su da kyautatawa, Allah ya yarda da su, su kuma sun yarda da shi, kuma ya yi

---

[1] **Tafsirin Ibnu Kathir,** na Isma'il binu Kathir, bugun Maktabatus Safa, Alqahira, 1423/2002, mujalladi na 1, shafi na 55.

masu tattalin gidajen Aljanna: ƙoramu suna gudana a ƙarƙashinsu, suna madawwama a cikinsu har abada. Wancan ne babban rabo." (**Suratut Tauba**: 100). To, waɗanda Allah ya yarda da su, ya tanadar musu Aljanna, ta ya za'a ce sun kafirta ko sun yi ridda?!!

**Allah ya yarda da su alhali yana sane da abinda yake cikin zukatansu:** Ya ce, "Lalle ne, haƙiƙa, Allah ya yarda da muminai a lokacin da suke yi maka mubaya'a a ƙarƙashin itaciyar nan domin ya san abinda ke cikin zukatansu, sai ya saukar da natsuwa a kansu, kuma ya saka musu da wani cin nasara makusanci." (**Suratul Fathi**: 18). Waɗanda suka yi wa Annabi (SAW) mubaya'a a ƙarƙashin wannan itaciya da Allah ya ambata su dubu da ɗari huɗu ne (1,400). Allah ya ambata cewa ya yarda da su alhalin yana sane da abinda yake cikin zukatansu, kuma ya kira su muminai. To ta yaya 'yan Shi'a za su ce Sahabban Annabi duka sun yi ridda bayan rasuwarsa wai sai mutum bakwai kawai? Allah wanda yake ganin abinda yake cikin zukatansu, da ya san za su yi ridda bayan Annabi, ya zai saukar a cikin littafinsa mai tsarki cewa ya yarda da su?

Babu shakka maganar Allah ba ta tashi. Shi ya ce ya yarda da su; su kuma 'yan Shi'a suka ce sun yi ridda? Subhanallah!! Wannan wane irin ɗanyen hukunci ne? Babu shakka a cikin wannan akwai jayayya da Allah da kuma ƙaryata littafinsa. Allah ya tsare mu da ɓata.

## Haƙƙoƙin Sahabbai a kan Musulmi

Sahabban Annabi(SAW), Allah ya yarda da su baki ɗaya, suna da haƙƙoƙi a kan ko wane Musulmi waɗanda ya wajaba a kiyaye da su. Haƙƙoƙin sun haɗa da:

1. Son su da ƙaunar su saboda Allah da Manzonsa suna son su.

2. Imani da fifikonsu a kan sauran dukkanin al'umma.
3. Imani da fifikon Abubakar, sa'an nan Umar, sa'an nan Usman, sa'an nan Ali a bisa wannan jeri. An ruwaito daga Abdullahi binu Umar(RA) yana cewa, "Mun kasance muna faɗi, alhali Annabi yana raye, Abubakar ne ya fi, sa'an nan Umar, sa'an nan Usmanu, sa'an nan Ali. Kuma Annabi ya ji hakan amma bai hana mu ba."[1]
4. Kamewa ga barin ambaton tuntuɓensu da kurakuransu, da nesantar shiga shara ba shanu dangane da saɓanin da ya afku a tsakaninsu.
5. Imani da alfarmar matan Manzon Allah(SAW) dukkaninsu, tare da cewa su Uwayen Muminai ne, kamar yadda Allah Maɗaukaki ya tabbatar a cikin faɗinsa, "Annabi ne mafi cancanta ga muminai bisa ga su kansu, kuma matansa uwayensu ne." (**Suratul Ahzab**: 6). Kuma a ƙudure cewa mafifitansu su ne Khadija da A'isha, Allah ya ƙara yarda a gare su baki ɗaya.

Ɗan uwa mai karatu, waɗan nan su ne haƙƙoƙin Sahabbai waɗanda ya wajaba dukkan Musulmi su kiyaye da su; amma 'yan Shi'a sun sarayar da su. Ba kawai sun sarayar da su ba, amma sun akkasa!

An umarce su da su so su, sai suka ƙi su!!

An umarce su da su fifita su, sai suka wulaƙanta su!!

An ce su kame ga barin ambaton tuntuɓensu, sai suka yi musu ƙazafi, suka dangana musu abinda ba su ji ba, ba su gani ba!!

Muna roƙon Allah da sunayensa kyawawa da sifofinsa maɗaukaka ya shiryar da su, ya arzuta su da tuba karɓaɓɓiya.

---

[1] **Sahihul Bukhari.**

*"Ya Ubangijinmu! Kada ka karkatar da zukatanmu bayan har ka shiryar da mu, kuma ka ba mu rahama daga gunka. Lalle ne, kai, kai ne mai yawan kyauta."* (**Suratu Ali Imrana**: 8).

*"Ya Ubangijinmu, ka yi gafara gare mu, kuma ga 'yan uwanmu waɗanda suka riga mu yin imani, kada ka sanya ƙulli a cikin zukatanmu ga waɗanda suka yi imani. Ya Ubangijinmu, lalle kai mai tausayi ne, mai jinƙai."*(**Suratul Hashri**: 10).